## Tambaya: Amma ai wata kila Bukhari, Muslim da wasun sun amince ne da hadisan wadancan mutane saboda ba su san hakikani akidarsu ba.

Wadannan malamai sun sadaukar da rayuwarsu ne wajen nemowa da yada hadisai, tare da bin diddigin rayuwar masu riwayar wadancan hadisan. Mafi yawan su suna da littafan *Rijal* (fannin hukunta aminci ko rashin amincin masu riwaya) da ake yabonsu da su. Duk da cewa zabinsu na fifita wasu mutane da wasu hadisai na nuna irin tsaurin ra'ayin akidar Sunni, sai dai duk da haka sun sami kansu suna amincewa wadancan 'yan Shi'a wadanda suka hukunta amincinsu. Wannan kuwa bai hana su kin yarda da akidarsu ta Shi'anci ba.

Don haka, yarda da cewa Bukhari, Musulim da sauransu ba su san hakikar akidun wadancan 'yan Shi'a masu riwaya ba, ya yi daidai da cewa **ba su da kwarewa** a fannin su!!!

## Tambaya: To amma me yasa ba su dogara da 'yan'uwansu Ahlusunna a matsayin hanyar riwaya ba?

Wata kila ba su kasance masu kuncin tunani irin *wasu* 'yan'uwamu da suka cije wajen lankayawa akidar Shi'a duk nau'o'in kage kage da karerayi ba ne. Za a iya fahimta daga abin da aka jero na takaitattun tarihinsu cewa, malaman Ahlusunna na da sun kasance suna jure sukan da ake yiwa wasu Khalifofi da wasu Sahabbai -bisa dogaro da dalilan tarihi da ba sa karyatuwa.

## Tambaya: To su ma 'yan Shi'a kan yarda da masu riwayar Ahlusunna a littafansu?

Matukar shi dan Ahlusunna mai riwayan ba a san shi da kin 'yan-gidan Annabi (s) *(Ahlul-bait)* ba, kuma aka yarda da gaskiyarsa, to malaman Shi'a na hadisi na karbarsa.

## Natija:

Gaskiyan al'amari shi ne cewa idan Ahlusunna suka ki yarda da 'yan Shi'a masu riwaya, to kuwa wani kaso mai tsoka zai bace daga *hadisansu* (Ahlusunna din). Don haka akidar Shi'a ta kasance kuma ta ci gaba da zama wata katangar karfe da ba makawa a kanta wajen wanzuwar tunanin Sunni.

**Don samun wasu bayanan a kan sahihin Musulunci, ziyarci wannan tasha ta yanar-gizo:**
***http://al-islam.org/faq/***

*v1.0*

*Ya ku wadanda suka ba da gaskiya! Ku ji tsoron Allah, sannan ku kasance tare da masu gaskiya*
(AlKur'ani: Sura ta 9, Aya ta 119)

# *Rafidi*
# 'Yan Shi'a Masu Riwaya a Cikin
# *Sahih al-Bukhari*

Da yawa daga malaman Musulunci na farko, wadanda aka yarda da gaskiyarsu da manarsu, sun kasance masu bin tafarkin Shi'a. Kuma mashahuran malaman Ahlusunna sun amince da abin da suka riwaito na hadisan Annabi (s).

A nan ***kadan*** ne daga malaman Shi'a da Bukhari ya fitar da hadisansu a cikin littafinsa na ***Sahih***. Idan muka hada su da wadansu irin su da Muslim ya fitar da hadisansu a ***Sahih*** da sauran ***Sihah al-Sittah*** hudu; na daga masu bin akidar Shi'a, to adadin zai karu sosai. Sai dai saboda takaitawa, an yi nuni da inda za a iya samun su a inda aka alamta haka da (*kitab*) a bayan kowane ***hadisi daya rak*** da aka ciro daga kowane mutum. Ana iya samun sauran a sashin jerin sunayen masu riwaya daga manyan littafai ko a software na *hadisi* mai amfani da na'ura mai kwakwalwa.

Mai karatu zai lura da kalmar ***Rafidi*** a wasu wurare daga abin da zai zo. Duk malaman Ahlusunna sun dace a kan ta'arifin ***Rafidi*** da dan Shi'a da ke suka da nuna kin amincewarsa da shari'ancin Khalifofin da suka wuce kafin Ali (a).

| | |
|---|---|
| 'Ubayd Allah b. Musa al-'Absi<br>*(Ya rasu a shekara ta 213 bayan hijra)*<br><br>*Sahih Bukhari* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih Muslim* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih al-Tirmidhi* [*kitab al-salat*]<br>*Sunan al-Nasa'i* [*kitab al-sahw*]<br>*Sunan Abu Dawud* [*kitab al-taharah*]<br>*Sunan Ibn Majah* [*kitab al-muqaddamah*] | ❑ "Abu Dawud ya ce: ya kasance mai matukar riko da Shi'anci. An yarda da hadisansa. Ibin Majah ya ce: Ahmad bin Hambali ya kasance yana nuna Ubaydullah ga mutane, kuma an san shi da ***Rafidanci*** (tsananin goyon bayan Ali), don haka ne ma ba ya bari duk wani mai suna Mu'awuyah ya shiga gidansa".<br>[*The Creed of the Imaam of Hadeeth al-Bukhari and of the Great Scholars from whom he narrated* (Salafi Publications, UK, 1997), p. 89 daga Dhahabi, *Siyar A'lam al-Nubala*, juz'i na 9, shafi na 553-557]<br>❑ "Mutum ne mai tsoron Allah, daya daga mahimman malaman Shi'a. Yahya bin Ma'in ya amintar da shi, Abu Hatim ya ce: ya kasance abin dogara, mai gaskiya. al-'Ijli ya ce: Ya kasance kwararre a kan AlKur'ani..."<br>[Al-Dhahabi, *Tadhkirat al-Huffaz* karkashin "'Ubayd Allah b. Musa al-'Absi"] |
| 'Abbad b. Ya'qub al-Rawajini<br>*(Ya rasu a shekara ta 250 bayan hijra)*<br><br>*Sahih Bukhari* [*kitab al-tawhid*]<br>*Sahih al-Tirmidhi* [*kitab al-manaqib*]<br>*Sunan Ibn Majah* [*kitab ma ja' fi al-jana'iz*] | ❑ Ya kasance mai gaskiya ***Rafidi*** kuma yana da hadisi a (***Sahih***) na Bukhari.<br>[Ibn Hajar al-'Asqalani, *Taqrib al-Tahdhib*, karkashin "'Abbad b. Ya'qub al-Rawajani"]<br>❑ Abu Hatim ya ce: Ya kasance shehin malami, abin dogara. Ibin Adi ya ce: Ya kan soki salaf (magabata). Akwai tsaurin ra'ayin Shi'anci a tare da shi. Salih bin Muhammad ya ce: ya kan soki Usman, na ji shi yana cewa: "Adalcin Allah ya fi karfin ace Ya karbi Dalha da Zubair a Aljanna, (wadanda su ne) bayan sun yi mubaya'a ga Ali, sai kuma daga baya suka koma suka yake shi". Ibin Haban ya ce: Ya kasance ***Rafidi*** mai kiran wasu (zuwa ga akidarsa) shi ya riwaito *hadisin* nan maicewa: "Idan kuka ga Mu'awuya a mumbarina ku kashe shi!"<br>[Ibn Hajar al-'Asqalani, *Tahdhib al-Tahdhib*, karkashin "'Abbad b. Ya'qub al-Rawajani"] |

| | |
|---|---|
| 'Abd al-Malik b. A'yan al-Kufi<br><br>*Sahih al-Bukhari* [*kitab al-tawhid*]<br>*Sahih Muslim* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih al-Tirmidhi* [*kitab tafsir al-Qur'an*]<br>*Sunan al-Nasa'i* [*kitab al-'iman wa al-nudhur*]<br>*Sunan Abu Dawud* [*kitab al-buyu'*]<br>*Sunan Ibn Majah* [*kitab al-zakah*] | ❑ Ya kasance ***Rafidi*** dan Shi'a, daya daga (mutane) masu ra'ayi.<br>[Abu Ja'far al-'Uqayli, *Du'afa al-'Uqayli*, karkashin "'Abd al-Malik b. A'yan"]<br>❑ Ya kasance ***Rafidi***, amintacce (*saduq*).<br>[Al-Mizzi, *Tahdhib al-Kamal*, karkashin "'Abd al-Malik b. A'yan"]<br>❑ Al-'Ijli ya ce: Ya kasance mutumin Kufah, kuma *tabi'i* ne, mai gaskiya. Sufyan ya ce: Abdul-Malik bin A'yan dan Shi'a ne ya ba mu labari. Ya kasance ***Rafidi*** a fahimtarmu, mutum ne mai ra'ayi. Hamid ya ce: wadannan 'yan'uwa uku, Abdul-Malik, Zurarah da Hamran, sun kasance dukkansu ***Rafidawa*** ne. Abu Hatim ya ce: ya kasance daya daga wadanda suka rungumi Shi'a tun farko; ya kasance amintacce, yana da hadisai masu kyau, kuma na rubuta hadisansa.<br>[Ibn Hajar al-'Asqalani, *Tahdhib al-Tahdhib*, karkashin "'Abd al-Malik b. A'yan"] |
| 'Abd al-Razzaq al-San'ani<br>*(Ya rasu a shekara ta 211 bayan hijra)*<br><br>*Sahih Bukhari* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih Muslim* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih al-Tirmidhi* [*kitab al-taharah*]<br>*Sunan Nasa'i* [*kitab al-taharah*]<br>*Sunan Abi Dawud* [*kitab al-taharah*]<br>*Sunan Ibn Majah* [*kitab al-muqaddamah fi al-'iman*] | ❑ Ibn 'Adi ya ce: (malamai) ba su sami matsala a *hadisan* shi ba, face dai sun dangana shi da Shi'anci. Ya kasance mutum mai daraja, ya riwaito hadisai kan darajojin 'yan-gidan Annabi (*Ahlul-bait*) alhali yana sukan wasu. Mukhlid al-Shu'ayri ya ce: na kasance tare da Abdul-Razzaq lokacin da wani ya ambaci Mu'awuya, sai Abdul-Razzaq ya ce: 'Kar ka gurbata taronmu da ambaton 'ya'yan Abu Sufyan!'.<br>[Al-Mizzi, *Tahdhib al-Kamal*, karkashin "'Abd al-Razzaq al-San'ani"]<br>❑ Ibn 'Adi ya ruwaito (*hadisi*) daga 'Abd al-Razzaq, cewa, "Idan kuka ga Mu'awiya a kan mumbarina ku kashe shi!".<br>[Al-Dhahabi, *Mizan al-'I'tidal*, karkashin "'Abd al-Razzaq al-San'ani"] |
| 'Awf b. Abi Jamilah al-'A'rabi<br>*(Ya rasu a shekara ta 146 bayan hijra)*<br><br>*Sahih Bukhari* [*kitab al-'iman*]<br>*Sahih Muslim* [*kitab al-masajid wa mawadi' al-salat*]<br>*Sahih al-Tirmidhi* [*kitab al-salat*]<br>*Sunan Nasa'i* [*kitab al-taharah*]<br>*Sunan Abi Dawud* [*kitab al-salat*]<br>*Sunan Ibn Majah* [*kitab al-salat*] | ❑ Ya kasance ***Rafidi*** amma amintacce... Malamai da dama sun amince da shi, a tare da shi akwai akidar Shi'anci.<br>[Al-Dhahabi, *Siyar A'lam al-Nubala*, karkashin "'Awf b. Abi Jamilah"]<br>❑ 'Awf ya kasance mai akidar Qadariya, dan Shi'a, Shedani!<br>[Abu Ja'far al-'Uqayli, *Du'afa al-'Uqayli*, karkashin "'Awf b. Abi Jamilah"]<br>❑ Ya kasance yana karkata ga Shi'anci. Ibn Ma'in ya ce: amintacce ne, Nasa'i ya ce: yardajje ne kwarai.<br>[Al-Mizzi, *Tahdhib al-Kamal*, karkashin "'Awf b. Abi Jamilah"] |